Lallai cewa Allah Maigirma da Daukaka ya nade mun kasa, sai da nagano daga bangon gabas zuwa bangon yamma , ku ma cewa lallai Al'umma ta Mulkinta zai kai inda aka nunamun, kuma anbani Taskoki biyu Ja da fara.

Daga Thauba -Allah ya yarda da shi- cewa Annabi ya ce: "Lallai cewa Allah Maigirma da Daukaka ya nade mun kasa, sai da nagano daga bangon gabas zuwa bangon yamma \, ku ma cewa lallai Al'umma ta Mulkinta zai kai inda aka nunamun, kuma anbani Taskoki biyu Ja da fara, kuma ewa Al;umma ta Mulkinta zai kai duk inda aka nuna mun, kuma anbani Taskoki biyu Ja da kuma fara, kuma cewa ni na roki ubangijina kada ya halaka Al'ummata da Annoba, kuma kada ya Dora akanta Abokin gabar wanda ba daga cikinsu ba wanda zai hallaka su, kuma Ubangijina ya ce: Ya kai Muhammadu, idan na hukunta kaddara ta to babu mai maida ta, kuma cewa na masa cewa Al'ummarka bazan Halaka su da Annoba ba, kuma ba bazan dora musu Abokin gaba ba sai daga cikinsu wanda zai kuma ya hallakasu koda kuwa duk Mutanen Duniya zasu taru don ganin bayansu, ta yadda wasu zasu rika kashe wasu kuma

[Ingantacce ne] [Ibnu Majah ne ya Rawaito shi - Abu Daud Ya Rawaito shi - Ahmad ne ya rawaito shi - Muslim ne ya rawaito shi]

Wannan Hadisi ya kunshi abubuwa kamar haka masu ggirma wadanda suka kunshi Al'amura muhimmai da kuma labarai na gaskiya, kuma wanda Maigaskiya abin gasgatawa ya bada labari, cewa Allah mai girma da daukaka ta tattare masa kasa har saida ya gano abinda Al'umma rsa zata Mallaka tun daga Bangon Duniya na gabas zuwa na yamma, kuma ya bada labari cewa Allah ya bashi Taskoki guda biyu, kuma hakan ya wakana kamar yadda ya bada labarin, kuma ya ce Al'ummarsa zata Mallake Mulkin Kisa da kuma Kaisar da duk abinda suke da shi na zinari da Azurfa da kayan kawa, kuma ya bada labarin cewa ya roki Ubangijinsa kada ya hallaka Al'ummarsa da da fari, ko kuma ya dora Mata abokin gaba daga cikin kafirai wanda zai wanda zai Mamaye garuruwansu kuma ya karar da Jama'arsu, kuma Allah ya amsa masa na farko, kuma ya amsa masa na biyun ma matukar Al'ummarsa ta nisanci sabani da kuma rarrabuwa, da kuma gaba a n tsakaninta, kuma Annabi ya jiyewa Al'ummarsa tsoron Hadarin Batattun Shugabanni da kuma Malamai; domin Mutane da su suke koyi cikin batansu, kuma ya bada labari cewa Fitina zata afku da kuma Yaki to cewa hakan zai ci gaba har zuwa tashin Alkiyamakuma hakika hakan ya faru kamar yadda, to tunda fitinar ta faru kuma ita ce take ci gaba har yanzu, kuma ya bada labarin cewa wasu daga cikin Al'ummarsa zasu koma cikin kafirai can garuruwansu da Addininsu, kuma cewa wasu Jama'u daga cikin Al''umma zasu koma shirka kuma hakan ya faru kamar yadda ya bada labari, don an bautawa Kaburbura da Bishiyoyi da Duwatsu duk da faruwar wadan nan Masifi da hadura, kuma wannan Jama'a ta gaskiya duk da karancintabata cutu da kaidin Abokan gabarta ba da

kuma wadanda suka saba mata.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/3337